**Interview 9: Maryama Ibrahim, Makitsiya**

Makitsiya (MK): Gaskiya ni na ma gode da aka yi min tambayai. Sunana Maryama Ibrahim. Tasawa cikin gari. Hilin sarki. Hilin sarki duk wanda ya je yâ ga gidanmu. I. Ƙwarai. Ke nan wanda aka ce tsakar gari ke nan su ne gari. Ko?
Interviewer (Int.): Mm.
MK: Madalla. Kuma ni Maryama Ibrahim gaskiya lokacin ina yarinya ban yi kitso ba amma yanzu da na shiga ɗakin miji. Irin wannan kana zamne, zaman banza, bisimilla dai, to sai aka maida tariya baya.
MK: Gaskiya dai na yi shekara hamsin da bakwai ko? Tun da dai da na san da haka nan da sai in taho da kart ki ta.

Int.: Madalla.
MK: Madalla. Madalla. Da aka yi muna aure muna zamne … kama ka san irin wannan zaman … ba ka son zaman banza, duk yaron da ka gani sai ka kama ka mâi kitso wata rana ya yi, wata ran bai yi ba, ke nan shi ke nan ha ka gwanance. Shi ke nan muka zage muna yin kuma gaskiya kitso alhamdulillahi. Wanga na zamani ne ba mu iya ba. Amman wanga, namu na tsohi, wallahi gaskiya an gode. Tun da dai an ci an sha an ma wani bukata. Ka yi bukata, ka ma ɗiyanka. Ke nan ai an gode. Wani ma ya zo kā mishi. Ke nan madalla. Ka yi bikin dange, ka yi bukin ‘yan uwa. Ka yi bikin sabba, ka je nan ka je nan ka je nan, to ai kuma alhamdulillahi. Sai à ce an gode.
MK: Ba wanda ya koya mumu, mu tsohi dubarammu ce. Dan duk yaro in ya zo, irin wannan na amarya ana yi maka hira, in kanshi ya … ya tsuhwa, sai ka kwance, yàu ba ka aikin komi. Sai ka kwance kana daddagulawa, kana daddagulawa, wata ran ya yi wata ran bai yi. Kala ana haka, ana haka nan ha munka iya. Ba wanda ya koya mumu… kai dubarak kanmu ce, ta kwakwalwammu ta koya mumu. Ko ba gaskiya ba? Tun da ba wani wuri ba muka je. Zamne muke cikin gida.

**Int**: Kuka koya.
MK: Muka koya. Sannu sannu muna yi bisa kanun yara ha muka iya. Ai an kai shekara talatin. An kai shekara talatin ana kitso.
**Int**: Mm.
MK: Ka ga tsinke, ni in ban yi kitso da wannan ba ba ni jin daɗi. Wannan tsinken daga Makka anka kawo mini shi.
**Int**: Tsinke ake ce mata?
MK: Tsinke. Zabarmawa su ce ‘tagi’. Mu ko tsinke muke cewa. In muka tsaga gashi tsaka, shi ke nan duk yadda kuma zamu yi …

**Int**: Mm.
MK: Da shi muke yi. E da shi muke yi. Duk inda za a lauya gashi da shi muke yi. E. wanga tsinke. Ka san abin da ya sa ba mu aiki da mashaci? Sabo da wani bai so a sa mishi mashacin wani.
**Int**: Mm.
MK: E.
Int: Sai ya zo da abinshi?
MK: Sai ya zo da abinshi. Amman wanga namu mu da shi muke yi. Amman, shi ka san haraka yanzu, da yake ba ka so ka sa gashin wani, sai ka ɗauko mashacinka. Can ma da ka zo sai mu ce ina mashacinka? Sai ka ba mu, mu shace kuma in kai zaka shace abinka ka shace. Ka ba mu kai. In ka ba mu kai, ka hwaɗa mumu. In ka hwaɗa mumu irin … wanda za mu yi maka, ka ƙare. Wannan daga Makka ma sai da anka kawo mini da takwas.

© Boston University

Int: Mm.
MK: Ka san akwai mantuwa.
Int: E.
MK: Iri iri ne. Wata rana in kai kana gaugawa, zaka gida, sai ka mance.
Int: Ee.
MK: Yau kuma, ka san wasu kuma in suna da bukata, sai su hana. Sai su ce ‘gaskiya ni ina son wannan tsinken.’ In ce ‘to’. Hanawa zaka yi? Ɗauki! Tun da akwai wani gida. Kuma in na je gida sai in ɗauka. Tun da yanzu takwas yake yanzu ya koma sauran uku. Yanzu ma wannan amma da kyal, na samo shi.

Int: Mm.
MK: Dâ cikin sakwat yake. To ban san ba yadda aka yi aka yadda. To daɗa wancan ban same shi ba, ba ni ma aiki da shi. Shī ne sai na ɗauko shi. E. Ka san kowa da abin da ya saba. Za ya tsaga da shi. Ka yi tsaga mai kyau. Ni na yi tsaga da wannan. Amman wannan in babu wannan, ka ma dole in ta kama sai mu yi da wannan amma ba dan muna jin daɗi ba. To kuma ka ga wagga, daga Agadas ake kawo su. Da wannan, ‘yan Agadas ke yo ta su ma.
Int: Ita ma tsinke ake ce mata?
KW: Ita ma tsinke ne. E. Ta kwanta kai. Ke nan tsinke ya zama iri iri…E. To ke wane iri za a yi miki? I? I? A’a hwaɗi dai wanda za a yi miki.
Customer: « *Wo kan kanu ni se.* » (Zarma for “*wanda ya yi miki kyau*”)

Int: Ko a yi mata tashin soji?
MK: A yi miki tashin soji dan su gani. A miki tashin soji dan su gani. E, manan. Tashin soji za a yi mata.
Someone Else: *D’accord*. Papi ! Papi !
MK: Yàu sa’annan .. Ka san ƙauye. Sojawa wata ran in suka zo ka san irin wucewa nan da suke yi.
Int: E.
MK: Yàu sai aka sa mishi tashin soji. E. E. Mu dai ba ruwanmu. Ba dai kâ biya ba? Kawai zance ya ƙare. E. Manan. Ba dai ka biya ba? Shi ke nan zance ya ƙare. He he he he … Zani raba shi tsaka. To yanzu kuma za’a hwara yin na gaba.

Int: Tô.
MK: Mm. Wannan za a dunƙule shi. … kira ka. To, za’a hwara kitso hwa!
Int: To.
MK: Yanzu mâi ne za shahwawa daga tsaka.
Int: Mm.
MK: Mâi, ga shi. Shi ko ke da unhwani. Tun da unhwaninshi, in aka tsaga, ka ga sai mu sa mai tsaka.
Int: Mhm.
MK: Ke nan in muka sa mai tsaka, kai bai hwarin wannan.

Int: Mhm.
MK: I. Irin wannan hwarin da yake cikin kai bai yi. Ke nan gashi zai samu ya hànzarà.
Int: Mm.
MK: Kuma gashi ba a tsiga shi kullum sai a yi wata yana kìtse.
Int: Mm.
MK: In ka kwance shi. E. Sai ka ga ya yi sama.

Int: Mm.
MK: E. Sai ka ga ya ƙaru. E. Ba kama irin wannan ba na wannan warai-warai ɗin. Kun gane? Kun ga mu in ana kitso hannu, nan bai cirewa.
Int: Mm.
MK: Nan, nan, kun gani? Ka gani? Ka ga ko?
Int: Mm.
MK: Ka ga gaba bai cirewa. E. To wancan ko wannan mirɗawa da ake, …

Int: Mhm.
MK: Sai ya cire. Mu ko nan ka ga nan bai cirewa. Sai ya ɗauka. Duk wanda ka ga gabanshi nan ya cire, to wânnan mirɗawa ce da ake. Mu ko namu ba a mirɗawa.
Int: Mm.
MK: Ke nan kuma gashi ya samu mai.
**Int**: Mhm.
MK: Kuma ba a matse shi ba ƙwarai.
Int: Mhm.
MK**:** To sai ya taso. A samu sai ya taso. To ka san kitso ga da, namu ka ga muna zumɓutun kaza

Int: To
MK: Muna yin tashin soji.
Int: Shi zumɓutun kaza yaya ne yake?
MK: Zumɓutun kaza. Haka ake maido shi nan. A yi zumɓutun kaza.
Int: Mhm.
MK: Kuma muna yin tashin soji. Ka san tashin soji? Haka muke yin tashin soji, nan, nan muke tsaida shi. E. Tashin soji ke nan. Sai mu tsaida shi tsakak kai. Duk mu tattaro sai mu tsaida shi tsakak kai. Shi ne tashin soji. Muna yin mali-mali. Shi mali-mali haka ake yin shi.

Int: Mhm.
MK: Duk a taro, a taro. Muna yin māyì mēs□rā. Mayi Mesira, shi ma kamam mali-mali yake. Amman in aka yi nan sai dai a karkato, a karkato, a karkato sai duk ya zo nàn wurin haka.
Int: Mhm.
MK: Shi ne Mayi Mesira. Muna yin zanen yawo. Zanen yawo shi kuma duk sai ya yi ƙasa. Ke nan muna yin mȍdâl iri-iri.
Int: Mhm.
MK: E. Manan. Haba !!! Bari wagga, bari zancen.

Int: Mhm.
MK: Mu da yake ka san mu kitsonmu na tsohi …
Int: Mhm.
MK: Sabo da bakin da azumi …
Int: E.
MK: Ya kai kwana goma sha ukku
Int: Mhm.
MK: Zuwa sha huɗu

Int: Mhm.
MK: Kama mata, mun hwara yi musu kitso. In ya kai ashirin watan ran, amma ga yanzu yana kai ishirin. Bakin da wata ya kai ishirin, can ma duk wanda kake ma kitso ka yi, wannan lokaci kaza zamu yi mai, wannan lokaci kaza za mu yi mai, ‘yan bariki su samdi dimashi garesu.
Int: Mm.
MK: Su wannan samdi dimashi nasu na. Wanda bai samu ba samdi dimashi sai dai ya yi haƙuri.
Int: E.
MK: Sai dai bayan salla.

Int: Mhm.
MK: Sabo da gaskiya kitso da muke yi bayan salla ma har ya hi na sallar yawa.
Int: Mm.
MK: E manan. Tun da ba ka iya game masu kitsonka. E. Tun azumi in ya kwan ishirin,
Int: Mhm …
MK: Shi ke nan mun hwara kitso ke nan sai daren salla.
Int: Mhm.
MK: Amman kuma ni daren salla ko i … ban zuwa ko ina.

Int: Mhm.
MK: Sai in yi zamne gida. Sssss … Duk wanda ya zo, ya hwarangaito sai ka yi mishi. Duk wanda ya hwarangaito gida sai ka zo ka yi mishi. Kingi wanda ba a yi ba kuma sai a dangana sai bayan salla. Dan sabo da gaskiya ni waɗanda nike ma kitso basu zuwa wurin wani (some speaking another language: “…sagoma.”- *apparently greeting someone*)
MK: Mm. Bayan salla ‘to daɗa ga mu mun zo. Shi ke nan sai a taho a yi.
Int: Mhm.
MK: Tun da sun sani gaskiya ba a iya gama ma kowa. E. Haka nan ne. ….Shekara da shekaru ana tattare ana yi.

Int: Mhm.
MK: E. …(Some woman speaking another language: *Yeka neyinyi?)* Sabadda in ka je ba mutum dai ba kake ma ba mutum biyu ba.
Int: E.
MK: Wanda ke…kanshi ke kwantacce, sai a hwara mâi. Wannan kuma ya kwance a hwara mai, wannan ya yi … a mai. Sai an yini ran nan. In ka ƙare wannan gidan kuma shi ke nan. Kuma gobe, sai ka nuhi wani wuri. Dajâ kowa ya sani kiliyan kinka ne.

Int: E.
MK: Shi ke nan. Ba wani matsala. Aaa, gaskiya akwai gajiya. Dan dai abin da mùtum ya saba. Kuma gaskiya mun riga mun saba. Akwai gajiya kama ka yini kana daka ne hwa in kana kitso. Kama ka yini jimƙa taɓarya ne kana daka. Haka ne hwa kitso. Sabadda … haka hwa ne. E. Kama ka ini kana daka ne. Aikin kitso wuya gare shi. Ga kama gaba nan, nan.
Int: E.
MK. E. Ka ga dan ba … dan ba ciwo ma kwana ta ke ko? Amman in wani wuri ne wane ita ta yi kwana in …. Ha ha ha ha ha…! Tawa suna da kitsonsu daban kama irin na bugajen nan.

Int: Mm.
MK: Wanda suke sabkowa.
Int: E.
MK: E. Amma su Marađi kitso duk haka ne .. Su ma Tawa suna da hawanya. Amma suna yin irin wannan na bugaje, Tawa.
Int: Mm.
MK: Mm. Amma su ma Marađi suna wannan, suna irin wannan kuma na zamani. Ka san dai kama kitson Tawa, in mun gani mun sani. Sai mu ce, a wannan na wajen Tawa ne.

Int: Mm.
MK: Kuma na Agadas, …
Int: Mm.
MK: In mun gani sai mu ce irin na Agadas na.
Int: Mhm?
MK: E. Sabadda điyan, irin wannan wanda suke yi, điyan, na Agadas sun hi yawa.
Int: Ee.
MK: Sun hi na Tawa yawa.

Int: Mm.
MK: Ka san in an kai wannan tulluwar, wannan wadda suke yi haka,
Int: Ee.
MK: To na Agadas, suna … bisa kan wani kuma sai su kawo wani su ƙara.
Int: Mm.
MK: E. Bisa.
Int: Kuna yi ma maza kitso?
MK: A'a. Mu tsohi ba mu ma maza kitso. Ha ha ha ha… Mu tsohi ba mu ma maz… amman bararoji suna yi ma maza kitso.

Int: Mm.
MK: E. Bararoji, su suna yi ma maza kitso amma mu ba mu yi ma maza kitso. Kama su Bararoji suna yi. Wannan tsakaninsu ne, al'adassu.
Int: E.
MK: Ko ba gaskiya ba?
Int: Mhm, mhm, mhm!
MK: Ka san kowa da al'ada tai.

Int: Mhm.
MK: Mhm. Su tsakaninsu Bararoji suna yi ma maza kitso.
MK: To, ƙarhi bai hi jiki ba. Wani wurin gaskiya muna cewa a ba mu wani wuri kuma sai mu dangana mu ce a ba mu abin da ka ba mu. E. Abin da ka ba mu sai mu yi aiki da shi.
Int: Mhm.
MK: E. Abin da ya sa ba mu cewa ka ba mu, ka ga in muka ce ka ba mu, in muka deba maka, in za … in kâ hi wannan hwa? Ke nan kā mā kanka.
Int: E.
MK: Yâuwa. Amman sai mu ce ka ba mu abin da ka ba mu. Abin da ka ba mu sai mu dangana. In muka ce ka ba mu in za ka hin haka nan.

Int: E.
MK: To ke nan ka ga ka maida kanka baya.
Int: E.
MK: Amman hwa in ka ce nawa ne sai mu ce “a’a”. Ka ba mu abin da Allah ya hore. Shi ke nan.
Int: Kitso da kuke yana da unhwani?
MK: Ƙwarai ko. Yana da unhwani. A gaskiya yana da unhwani. Allah sa albarka. Tun da an ci an sha, an yi bukata. Ko ba gaskiya ba?
**Int**: E.
MK: Wani ma ka mishi. To. Ke nan an yi unhwani.
**Int**: Mm.